https://chat.whatsapp.com/DGIo9iiSjlgJPPqFHNtddH

*♡SPECIAL☆*
_Ta daban_

*_بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيم_*

_Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai._
~Na Maryam Naseer Mirrah~
_AMMEY LAYLERH_
Page 1&2
_ƊAN ƊANO_

*NA'EEMA SULAIMAN SARAUTA*. _NIMCY LUV_ Ban manta kalan gudun mawar da kika ringa bani ba a littafi na na baya wato MIKIYA. TO haka za wannan ma da Salonta labarin ze fara SEY MA SHA ALLAH.Na sadaukar miki da wanan littafin, this novel is for you my humi darling, my Mummy'na, my support system, my role model, i love you_

*_Special Thanks to:_*
Masoya masu bibiyana ina alfahari daku a ko ina a kowacce duniya kuke
Love you all 💞💖💘💗💝
♡♡♡♡♡♡♡

The official trailer for *SPECIAL* {Ta daban} (2025) introduces Novelist to a chilling😄💃, suspense-filled Power Romance thriller set in an isolated, post world. Directed by MARYAM NASEER MIRRAH *AMMEYLAYLERH* SHEIKH JURAIJ THABIT JT follows.
*♡SPECIAL☆*must evade capture while uncovering hidden truths about her past and her connection to the cult's terrifying leader. The trailer teases
In a world where trust is a luxury and survival is the only rule.

Alhamdulillah masoya na Asali am back dawo muku da wani fitacce kuma ƙayatacce ƙasaitaccen labarin dazai ƙayatar daku💃, Bazan iya misalta muku meya ƙunsa ba sai inhar kun biyo alƙalamin AMMEY LAYLERHbAnan ne kaɗai zaku fashimta inane alqamin ya dosa🪷, fatar baku manta da ƙayatattun littatafan nan nata ba irin su.
*MIKIYA*
*KAREN BANA*
*JALAAL AREEF*
*ƘAUNA BIYU*
*SANYI YA HAIFA WUTA*
And Ongoing
*♡SPECIAL☆*
Fatan baku manta da yadda kuke nishanɗan tuwa da duka littatafaina na baya ba. Iyaka waɗan da suka karanta littafinta na MIKIYA to kuwa sune zasu fi kowa bada yadda waccen tafiyar ya kaya. Se dai wannan ma is not free book shima yazo ne a paid amma kafin nan akwai free page da zan ba *MASOYA* Masu bibiyana.

♡♡♡♡♡♡♡♡♡♡♡♡♡♡♡♡
*_KADUNA MARAFA_*
~012 Alongside films shot~

Cike ƙaton hall ɗin yake da mutane babu ko masakar tsinke.kowa ka kalla zakaga fuskansa na ɗauke da annurine. Dan kuwa kalla ɗaya zaka ma fuskokin nasu ka gane lallai suna cikin farin ciki ne matuƙa. Se dai wasu tsirari daga cikin jama'ar dake cike tab da hall ɗin suka soma kallar wrist watch ɗin dake ɗaure da hannayensu suna jan tsuƙa can ciki ciki. Wasu kuwa suna a cikin yanayi ne na shiru fuskansa suma yana fara sanjawa zuwa na damuwa. Domin kuwa idan har akace yauma Babbar jarumi kuma fitacciyar ƴar wasan Hausan nan wato *DIAMOND MEESHERH* ba zata samu halartar wannan shooting trailers ɗin ba Lallai kuwa da akwai babbar damuwa. duka mutanen dake zaune a hall ɗin zaka kalla lallai yakai ya kawo ya kuma taka wani matsayine tabbas, ko daga yanayin murjewan jikkunansu da kuma uwa uba tsarin da hall yake da.

Wani shahararren tallane na ADD companies Wanda manyan ƙusoshi suka haɗaka wajen gina shi, Tsaye tsammm shi kansa shugaba a companies ɗin ya miƙe ganin wasu har ransu ya soma ɓaci. Ehhhh lallai tabbas kuwa da haushi ace yau har kimanin kwanaki uku kullum a jere suna taruwa iwar haka amma haka suke bajewa ba tare da an gudanar da TRAILER na ADD companies ɗin ba.
A dai-dai loƙacin ne kuma wata farar mota samfurin ƙirar Toyota Highlander ta yi parking a harabar hall ɗin. Cikin yanayi na sauri² wata farar matashiya amma ba can ba ta fito daga cikin motar tana sanye cikin wani baƙar
pleate skirt sai farar oxford shirt wadda ta ɗora maroon suit a kai,wuyanta saƙale da tie se silver band ɗin dake kanta, gashin kanta wanda ya ji gyara an ɗaureshi cikin pony rail ya zubo har gadon bayanta. ƙafafunta sanye cikin baƙaƙen sneakers. A kuma daidai loƙacinne hall ɗin ya ɗauka wani kalan ihu na tarin masoyanta, har wasu na tsalle wanda suke daga waje basa da ikon shiga ainihin inda za'a gudanar da Trailer ɗin.Hotuna wasu suka fara ɗaukanta wasu na aikin video wasu na ɗaga takardu masu ɗauke da sunanta me hadɗi da tallar ADD companies.ɗaya daga cikin security female ɗin dake zagaye da wurin ne tayi saurin isa ga DIAMOND MEESHERH tana saƙala mata Symbol na tallar da zata gudanar.

Cike da mutsuwa take tafiya Fuskarta rufe da mask, ta rufe fuskar ne kuma saboda bata son takurawar jama'a, duk da kasancewarta mutum me nuna so da ƙauna ga masoyanta, Fuskanta da kai tsaye ba'a gani ta zare mask ɗin dake kan fuskan nata ganin ta faranta wa masoyanta Rai. Wani twisting na ihun murna mutanen suka sake saki suna jin ƙaunarta na sake ratsasu. A natse cikin wannan ɗan banzar izza da mulkin da duk wani ahali daya kasance ɗaya daga cikin ahali na *JEDAANS POWER MENTION* to kuwa kowa yasan *_Respect and peace_* ake ƙiran duk wanda ya fito daga wannan Ahalin. Tafiya taci gaba dayi harta dangana da kan stage na hall ɗin. Tun kamin ta kai ga shigar manyan mara masu gwara kan nera yaran ajebor suka ɗauka wani kalan ihu suma harda ma waɗan da suka ɗan manyan ta bi ma'ana dattijai masu rukunin ADD companies kenan. Microphone ɗin da wannan macen security ta farko ta sake maƙale mata ne ya sanya sakin kyakkyawan murmushi tan nan me kyau. Nan aka soma gudanar da duk abinda ya tara sun bayan ta nemi afwan su akan cewa wani uzirine me girma

ya ɗan riƙe ta.  Seda ta ɗan rumtse idanunta sakamakon tunowa da musabbabin hanata fitan kai tsaye. Bayan masu camera's sun gama haskata kana suka buƙaci data ɗan gudanar musu da show haka koda ba me yawa bane. Cike da wannan fara'an da son farantama masoyanta Kamar yadda suma suke faranta nata ranta ta soma gudanar musu da wani zazzafan show ɗin daya sake haukata ƙaton hall ɗin. tana tsaka da gudanar da show ɗin ne kuma Moh Saif Ameen turaki ya bayyana shima cikin hall ɗin nan sukaci gaba da gudanar da show ɗin a tare. Sosae yanayin ya musu daɗi Kamar yadda suma fam nasu suke  jin daɗin show ɗin na yau, dan burin ransu ne ya cika A  yau gasu ga manyan masoyansu,Suna gudanar musu da show a tare wato *DIAMOND MEESHERH SAMEER JEDAANS* da kuma *MOH SAIF AMEERN JEDAANS* Cike da jin daɗi da kuma farin cikin kasancewar su a tare  Masoya suka shiga ihun murna. Tsitttt kuma hall ɗin yay sakamon  tsaya wa da sukay suna  kallon masoyan nasu.

Ihun murna masoyansu sukaci gaba dayi haka har taron ya tashi, Moh Saif ne ya zagayo ta inda Diamond Meesherh ke tsaye bayanta zagaye da security. Hannunta ya kama bayan mutane sun gama murnar yin pisc dasu kai tsaye har inda tay parking car nata ya kaita seda ya tabbatar da shiganta kana shima ya koma yana jan tashi motar ya rufa mata baya. Sun zo daidai shan kwanar
Mobil filling station na  round about wani shegen goslow yay blocking na hanyan.

Ɗan tsuki kaɗan tayi tana jin gundura da zaman motarn baki ɗaya hakan ne kuma ya sanya Meesherh Jedaans fita don ganin ko me yay blocking hanyan har haka. Duk da kasancewar face nata rufe yake cikin mask amma hakan be hana wasu ƴan mata biyu da suke cikin napep kasa gane taba.      Wacce face nata ke waje tana leƙen woje ta window'n napep ɗin ta furta "Laaa A'isha  kalla can ki ga  kamar Diamond Meesherh Fa?" ta faɗi cike da ɗaukin ganin babbar jaruma kuma sananniya a duniya.  Da sauri wacce aka ƙira da A'ishan itama ta dawo da kanta setin inda ake nuna matan, "Wllh kuwa Rumaisa itane da da gaske!"  Ta faɗi tana ɗan zaro idonta woje alamun mamaki.

Cike da zumuɗi wacce aka ƙira da Rumaisa ta sake furta.

"Kinga tashi don Allah muje muy photo"

Ɗan numfasawa A'ishah tayi tana sauƙe numfashi tare da duban Rumaisa tana me furta.

"Ki na ganin zata  yarda kuwa Rumaisa? Karfa ki manta cewa Diamond Meesherh ⭐ Cikakken sunanta *Meesherh Sameer Jadeens*   wannan shine full name nata  bayan haka kuma role models da duniya jeji da ita gaba da baya.  A yanzu haka ita kanta Meesherh Jadeens na ɗaya daga cikin world billionaires da duniya ke ji dasu  ta  gama zama cikakkiyarn attajira a loƙacin data mallaki manyan company's dake tashe a ƙasashe daban daban. Bare azo ga ahalinta kai tsaye kuma. Kana ƴa ce ga Sameer Jedaans  Kuma sanin kankine kamar cewar Meesherh Sameer itace zuciyar duka alhalin Jedaans baki ɗaya! taya kike tunanin ma zata tankamu bare ma harta kula mu?.Sannan kuma kin  manta cewan duka wasu campanies da zaki kalla na *MEESHERH LUXURY PRODUCT* Ina nufin M.L.P fa nata ne ko kin manta kamfanine da suka lashe maƙudan dukiya wajen ƙirƙiran campanies ɗin kawai.
Wanda bako wanne  kamfani yasamu irin wannan shaharar ba bayan latex cars da campanies nata suke ƙera ma duniya. Kana tana da hannun jari da wannan shegen campanies ɗin nan da ake sarrafa laptops, iPhones da suke ƙerama duniya da duk wasu nau'o'in na'urori kolo daban daban. Wato babban Ɗa ga JEDAANS kuma me Jedaans ɗin baki ɗaya wato *SHEIKH JURAIJ THABIT JADEENS*"

A'isha ta ƙarishe maganan tana fesar da numfashi me ɗan zafi daga bakinta.

"Wllh naji mutane kam na yabonta sosae A'isha wllh kamar ba ruwanta"
Sake fuskantar Rumaisa A'ishah tayi kafin ta furta."To shikenan mu gwada sa'ar mu! Allah yasa mu dace" ta furta suna ɗaukan eskis wa me napep ɗin. Tana dab da shiga motan nata da ɗaya daga cikin securities ya buɗe mata Cike da ɗoki da zumuɗi Rumaisa ta isa gareta.tana me furta "Amm.... Am don Allah Sis kozan.... Securities ɗin da suka dakatar da itane suka sanya Jikin Rumaisa yin sanyi sosae tana jin tamkar ta muzanta kanta, kana tayi kutse wa matsayin da tasan ita bata isa takai koda kwatar wurin bane. "Ku..ku yi haƙuri amma dama photo ne kawai zamu ɗauka dama" Ɗaya daga cikin securities ne ya sake doka musu tsawa cikin buɗaɗɗiyar muryarsa yana furta.
"ku ɓace min a wurin nan, ko kunga Hajiya tayi kolo da ƴaƴan talak....
Shiru yay sakamon tsawar da shima Meesherh Jedaans ta kotsa masa.
A tare securities ɗin duka suka juya suna kallonta. Mask da kuma Baƙin shade ɗin idonta ta zare tana watsawama securities ɗin kallon me yasa kunnenku har abada baya ji?.
Kana ta juyo da dubanta zuwa ga ƴan matan biyu fuskanta ɗauke da wannan murmushin nata wanda yake ƙaramar fuskanta kyau. Ta sakar musu tana amsan woyan dake riƙe a hannun A'isha ƙurar OPPO tana furta. "Ayya I'm a so sorry sister's Password fa?" Ta faɗi cikin muryanta me shegen daɗi. Jikinsu har rawa yake suka bata password na woyar ta buɗe tana nemo camera na woyar. kana ta matso tana shiga tsaƙiyansu ta dafa duka shoulder's na ƴan matan tana ɗaukan su photo. Kuma duk ta ɗauka ne suna kallonta irin na mamakin nan lol.
Wayar ta sauƙe bayan ta gama musu pisc ɗin kana ta koma motarta bayan ta mayda mask ɗinta fuska, Har driver na shirin tada car ɗin tayi saurin dakatar dashi magana tasa ya mata da ƴan matan ID card nata me ɗauke da phone nata da kuma full address ta basu kana ta amshi phone na ɗaya daga cikinsu tana faɗin idan ta sama free time haka zata neme su.
Mamaki, Al'ajabi sune suka bi suka sake daskarar dasu Rumaisa a wurin, wuri kuwa tuni ya cika sedai ita kamm har tayi saurin ba driver umarnin suje kawai don hayaniyan mutanen harsun fara hawan mata ka.
Kai tsaye katafaren dogon ginin da kai tsaye zamu iya ƙura da da aljannar duniya suka nufa, Mention ne babba domin kuwa *_Respect and peace_*
Gidane babba wanda a yanzu haka yana daga cikin best and top mansions dasuke most expensive and attractive a cikin faɗin Nagerian kai harma da duniyan baki ɗaya.Faɗin irin tsarinsa da haduwarsa ma ɓata time ne abinda kawai zance na sani shine cewan gidane haɗaɗɗe tsararre kuma ƙerarren dayake gari guda a girma.

Sam bata leƙa ko inda Mah take ba kasancewar a gajiye ta dawo, kai tsaye samanta ta wuce kasancewan dama bata tarar da kowa ba a parlour'n. Bata fito Sai bayan anyi sallar Isha'i kana ta saƙko daga saman stairs nata.A loƙacin dakkanin jama'ar gidan suna kammale ne a babban parlour'n gidan domin yin dinner. Kai tsaye inda Abbie'nta ke zaune ta nufa fuskanta a ɗaure taki sakinta don ma gudun kada wani daga cikin mutanen parlour'n ya kawo mata wargi.B Tana sanye ne wannan karon cikin wani Turkey gown Wacce ta fidda shape ɗinta kai tsaye sosai, inda ta yi rolling gyalen a kanta.Ba laifi kuma tayi kyau sosai cikin shigar illa kawai shape ɗin ta daya fita sosai ne kawai matsalan shigan nata.

Iyaka iyayensu mata ne a wurin kai tsaye jikin Mah ta faɗa tana maƙaleta "Mah yau duk a gajiye na dawo amma ko nemana bakiy ba" ta faɗi tana tura bakinta gaba. Bakin data tura matan Mah ta ɗan mirza ba da yawaba "Ni kuma duk yau na wuni aikine gyaran room na babyn daddy" Sautin tsuƙin da aka jane ya sanya su su duka kalla duk da kuwa sun riga da sun san ko wace ɗin tay kai tsaye. Basu wani tanka ba haka har metres ɗin dake aikin ta na saving kowa dinner tazo ta jerema kowa abinda yake so.

pancake breakfast ɗin da ta fi so with honey aka jere a gabanta, kasancewar harta da metres na gidan sun san Diamond Meesherh bata cika son abu me nauyi ba. Ta gefen idon taga sadda ya shigo parlour'n,Nan parlour'n ya sake ɗaukan shiru kowa na rige rigen gaida babban yayan nasu wato *SHEIKH JURAIJ THABIT TURAKI* Kanta ta ɗauke ko kaɗan bata nuna wata alamar ta kula da shi ba har kuwa loƙacin daya kai zaune daidai kujerarn dake pacing nata. Cikin sauri Annie ta miƙe fuskanta babu alamun Rahman ko kaɗan. "JURAIJ tashi dawo nan!"
Wani irin Shiru daƙin ya ɗauka na wani ɗan loƙaci kafin ka fara jin sauƙe numfashin wasu mara sauti sosai Domin kuwa kowa ya riga da yasan halin Annie akan rashin son zamar lafiyanta, da kuma kalan tsanan da tama Meesherh ɗin.
Me ran ƙarfe Jedaans Turaki na shanu dake dap da shigowa parlour'n ne ya ƙarasa shigowa cikin ɗan hanzarin Sameer Jadeens ya ja may Sofa yana kaiwa zaune. Wani ɓoyayyen numfashi Sheikh juraij ɗin ya sauƙe mara sauti numfashin sa na cunkushewa da bugun zuciyarsa, ba tare da yace komi ba ya miƙe da niyar komawa inda mahaifiyarsan ta bashi umarni Jedaans Turaki na shanu ya ɗauke fuskansa daga kallon bugun zuciyar nashi Sheikh.
"Koma zaune a idda kake"
Haka kowa yaji sauƙan muryan tsohon, Mah ce ta miƙe da niyar barin wurin domin ita zuciyanta bame iya jure ana wulaƙanta nata bane ta ƙyale. Shirun kuma da tay tsumawa kawai namomin jikinta keyi ta kuma yunƙuro ne da niyar medama Annie da zazzafan martanin da ke kusan halaƙa nata zuciyan Muryan tsoho Jedaans ya katse mata tunani. "Kin yi lonch da zaki tashi ne Zulfa'u?" Haka ta sake tsinkayar Muryan tsohon a karo na biyu. Chakkk ta tsaya ba tare data juyo ba ta furta. "Ina da buƙatar na kaɗaice kainane kawai Baaba!"
"Da akay mike mene?"
Kai tsaye ya wulla mata tambayrn shima. Shiru tay taƙi bashi amsa zuciyanta na sake turara da wutar tsanar duk wani JINI daya danganci Annie. wata kyakkyawar ijiyar zuciya me nauyi tsohon ya kawo yana jin abu ɗaya shine zeyi maganin duk wannan matsalan {*AURE*} zuciyarsa ya furta mashi idan yace zuciyarsa seda yau tsalle to kuwa tabbas beyi ƙarya ba. Wani bahagon murmushi kuma ya saki daidai da Shigowan zaratan magidan tan gidan guda biyar. THABIT JADEENS, AMEERN JEDAANS,SAMEER JEDAANS,JAMAAL JEDAANS,EL-MUAZ JEDAANS. A natse suka ƙara shugowan kowa na nemar inda ya dace ya zauna, Baaba suka fara gaidawa kafin daga baya nan ɗaya bayan ɗayan yaran gidan suka fara gaida iyayen nasu cike da girma mawa. Wancan maganar tuni ya fice suna me fuskantan yin dinner nasu kawai. Sedai a wasu zukatan lamarin kuwa be shuɗe ba yana nan daram matankwacin yadda ake ɗora kwarya a gurbinta.
Sheikh juraij Jedaans da yafisu ƙarfin halin danne abu a zuciyarsa ne ya fara miƙewa zuwa balcony na side ɗinsa.

Idonsa toshe da bakin gilashi ajiyan zuciya ya saki abinda ya danne ƙirjinsa da daɗewa  yaji ya yana ɗan lafa masa yana jin ɗan  sassaucin ba kamar ɗazun ba. Shiru yay yana tsaye daga jikin doguwar Sofa irinta hutawar nan, lumsassun fararen idanuwansa ya buɗe yana fesar da wani abu me kama da  ɓacin rai. Mohan Sameer Jedaans da tun ɗazun yake tsaye a bayansa ne yay gyaran murya domin lura da yay kamar juraij ɗin ma be san da tsaiwarsa wurin ba. Wata coffee cough ya janyo ya ajiye  seti da inda Juraij ɗin ke tsaye yana ɗora ƙafansa kan ɗaya yana tallafar kuncinsa da left hand nashi.  A hankali cikin tsanani na nisan kiwon dayay a duniyar tunani  ya buɗe fararen idanuwansa da haskensu ya ɗan ragu na ɓacin ran daya ɗan wanzu  ya sauƙe akan Mohan ɗin wanda babu kamannin kowa akan fuskansa kai tsaye sena Diamond Meesherh Sameer Jadeens. "Yaayaa sheikh beci ace har zuwan yanzun kana barin damuwowi irin haka suna brain out naka har haka ba" Mohan Sameer Jedaans ya furta yana jin shima ƙunci da damuwar gakan na sake mamaye zuciyarsa.

Bayansa ya juya may don a yanzun baison yin magana da kowa hakan da yay ne ya sanya Mohan fahimtar mi hakan yake nufi.  Wani abu me raɗaɗi Mohan ɗin ya haɗiye kafin ya buɗe bakinsa ya furta. "Idan Yaayaa Sheikh ya dawo daidai ko zuwa safiya ne inason magana da shine kai tsaye. Hannunsa yaɗan wara may alamun yaje yana jin sadda Mohan ɗin yay may nisa da barin balcony ɗin ya buɗe fararen idanuwan san yana me bin bayansa da kallo.

★

*Meesherh*

Bayan bajewan kowa a dining room ɗin ne suka tattauna irin maganganunsu da ya shafi iyaka su tsakaninta da tsohon daga haka tamay sallama tana wucewanta zuwa nasu ainihin  Passes ɗin.

Tana dap da shiga Annie kuma na kawo kai zata fito daga sassan da tayi niyar janye wa amma da taga matar ne se kawai ta sa kai tana tafiyar ta. Daga inda yake tsayen yake kallar komai hakan yasa shi ɗauke idonsa akansu yana jin wani abu me kama da gazawa ko kasawa na son wanzuwa a ransa. Ganin yana wa'azi domin al'umma dama duniya su zauna ƙalau da juna se gashi a familynsa sam hakan yana ƙoƙarin ruguzuwa.  Zuciyarsa yaji tana sake cunkushewa da wasu tarin abubuwa maban banta. Wasu shuɗaɗɗun al'amurra da suka jima da shuɗewa na ƙoƙarin zeroying mind  nashi.

Zaune takai gefen bed nata tana duba tarin reports na acct histories na duka companies nata tana ganin yanda komai ke sake haɓaka kansa, Wasu rubutu masu ɗan tsayi tay kafin ta miƙe akan laptop ɗin tana faɗawa toilet. Da alwula ta fito duk da kasancewar tasan ba sallah zatay ba amma kuma hakan ya riga ya gama zama ɗabi'anta tun tana ƙanƙanuwanta, tun tana ƴar renonsa shi da kansa ya ɗora ta akan duka tsarikansa. Kafin wani rubutaccen Al'amari me kama da walƙiya yazo ya gitta wannan shaƙuwar. Ko bayan faruwan komai taso ta yafitar duka al'adunsa sedai wasu kammm samm basu yakitun ba.

Saurin kawar da wancan tunanin tay tana tofe ko ina nata da addaan bacci.

A hankali Moh Ameern ya rufe ƙofar ya mayar sam babu ƙarar takun sa ko kaɗan akan floor ɗin, shi yasa kuma bata lura ya ƙaraso har gaban gadon ba kasancewar ta riga da ta kashe bals, bata rufe bedroom nata sauda dama amma kuma saran shigo mata room Kai tsaye da Moh Ameern ɗin ya kowa ne ya tilasta fara rufe room nata. Ko a yau ɗin ba mantawa tay bata rufen ba bayan fitar wata mets data biyota da cup me ɗauke da tea party bata na al'ada wanda shi kansa hakan taso yakitarwa sedai shima hakan yaki yakituwan.  Zamansa ya bakin bed ɗin

harma yana ƙoƙarin yaya blanket data rufa dashi shine ya farkar da ita daga gajeren bacci daya soma ɗaukanta kasancewanta mutum bame wuyar bacci ba haka kuma bame wuyar tashi ba.

Zaune tay saurin tashi tana kunna bedside lam ɗin dake gefen gadonta. Ta cikin ɗan hasken daya haska room ɗin ba da yawa ba ta nuna may hanyar fita a room ɗin tana me furta "Out Moh!!!" Cikin mugun ɓacin rai. Hannunta yake ƙoƙarin ganin ya lalabo "kinga rilax beb wani aikine yanzu aka turomin ta email address shine nake son nuna miki ba komi ba!"

Ya furta yana sake matsota, "Amma get out nace ma ko?, Ko WhatsApp ba amfaninsa hakan ba da seka ratso har room nawa? Kodan kawai kaga ina baka fuska shine a kullum kake sake bayyanar min da munanan halayenka na ɓoye?"

Ta furta da ƙarajin da badan ace ƙofa ce mara fidda sauri da kuwa tsaff kowa da kowa dake a side ɗin na iya jiwota. A sanyaye ya miƙe yana kama hanyar barin ɗakin. Ak'adansa ne kullum se yayi zagaye don tabbatar da komi na dede ko wanne matashi kuma na a makwancinsa. Yazo seti da window'n room nata yaji kamar ihun faɗarta, Hakan ya sanya shi zagayowa domin ganin komi ke faruwa duk kuwa da yadda zuciyansa ke gargaɗansa akan aikata hakan. Gilmawar inuwar kawai ya gani amma kasancewar mutum mai kaifin brain da kuma karantar halayyar ɗan adam kai tsaye ya gane ko wanne ya gilma ɗin.

Dummmm haka yaji kansa ya bada sautin yanajin zuciyan sa kamar ana sauƙeta a ƙasa, sassan jikin sa kuma tamkar ana kwara musu ruwan suna suna tashi a aikinsu. Da ba ya baya ya shiga komawa cikin kamalallar takunsa har dogon wandon farar shaddar jikinsa na neman shatalarsa. Da bibbiyu bibbiyu idonsa suke gani haka harya kaishi ga dangana da sashinsa, jagwab ya kai zaune amma kuma cikin nutsuwansa da kuma cikakkar kamalarsa yay hakan.

"Kamar Yadda Allah yake juya dare zuwa Rana. Ya Ubangiji na roƙe ka ka juyar da damuwarmu zuwa farin Cikinmu🙏 domin na san cewa ƙaddarorin yanzu ne suka fara! Yanzu ne LABARINMU zai soma......"

*By Ammeylaylerh*

08104493215

_Tofa Fan's shi kuma wannan nashi salon kenan, da wannan muka fara_

_Jedaans Mention yau kuma ta kansu Labarin ze soma_

_to my fam nawa idan kunason ayi tafiyan daku seku biyo NI AMMEY LAYLERH domin jin yadda wannan zazzafar tafiyar zata kaya_

_Karfa ku manta sunan wannan littafin TA DABAN, to wai ma wace ta daban ɗin kowa dai a karan kansa yasan cewar ai shi na daban ne, to kuma ga wata AMMEY'NKU LAYLERH tace wai ita ɗin SPECIAL ce ta daban...._

_to ya kuke kallon wasan ze kaya? Ya kuma kukaji salon rubutun wannan karon? _

_Ni ban ze ce ma kowa komi ba kawai dai nasan zance mu haɗu a kashi na gaba domin jin yadda zata kaya_

https://chat.whatsapp.com/DGIo9iiSjlgJPPqFHNtddH

*♡𝕋𝔸 ***DA***𝔹𝔸***N***☆*

_𝘚p̶eci̊ɑʟ_

*_بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيم_*

_Da sũnan Allah, Mai rahama, Mai jin ƙai._

***Na Maryam*** Naseer ɱi̊rrɑh

_AMMEY LAYLERH_

BOOK ONE............✍
Page 3&4

♡♡♡♡♡♡♡♡♡♡♡♡

_015/01/2025_

Paid Book

*Maman Ihsan tawa duka wannan page ɗin na sadaukar miki dashi kiyi yadda kike so dashi idan ma kinso ki hana kowa ciki kuwa har dani AMMEY LAYLERH*

*MIKIYA*
*KAREN BANA*
*JALAAL AREEF*
*ƘAUNA BIYU*
*SANYI YA HAIFA WUTA*

✯ *~🌠 JAJIRTATTU WRITER'S ASS.... 💫~*

_Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa

su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi_.✏️

# New Year's
# □he tension □n □his Scene
# SoulmateVibes
# DeeplyInLove
# TogetherForever
# UnbreakableBond
# Endless Love
# SilentLoveAffair
# HiddenHeart
# ForeverAndAlways
# lOVE ROMANCE BABY
# a.k.a Ammey Layerh
👇
https://t.me/+ISpf1Iql0GwyNmJk

Duk me neman AMMEYLAYLERH ganan link nawa na Telegram Wanda kai tsaye idan kabi link ɗin ze dinga kaika ga post namu kai tsaye.
👇 https://www.facebook.com/share/1A1gMDViUG/

Sannan kuma ganan na facebook don samun post nawa kai tsaye shima.

♡♡♡♡♡♡♡♡♡♡♡
.... Tun da ta mai da doorhandle ɗin ta koma ta jingina da jikin ƙofan abubuwa da yawo na son dawo mata. tun da ga loƙacin da tafiyar su tasha banban da juna wacce wata shuɗaɗɗiyar Ƙaddara tazo ta ratsa tsakani. Haka kuma idan taso wannan ita dai ƙaddarar itane zata zo ta sake haɗe giɓin data riga da raba shekaru da ɗan dama.A zahirance duk inda Kalmar KADDARA take to kuwa kowa yasan kalma ce dake motsa zuciyar ko wanne bawa domin kuwa tabbas wannan kalmar ta KADDARA kalmace me girma da faɗi wacce ta ƙunshi abubuwa masu yawan gaske. domin kuwa Rayuwa da ƙaddara a tare suke tafiya tamkar ƴan uwa juna.haka kuma kowacce rayuwa tafe take da nata salon ƙaddarar.
Idan har bawa zeyi haƙuri wajen jure wannan tarin ƙaddarorin da suke jerin gwano a cikin kowanne rai mai numfashi game da duk abinda ALLAH ya riga da ya ƙaddara a cikin rayuwarshi,To kuwa duk ALLAH Ya zaɓa maka shi ne mafi alkhayri agareka.
♡ Wani kalan Runtse rinannun idonta tayi sakamon kanta da taji ya wani kalan mugun sara mata da tsanin ciwo. Zaune takai bakin bed haryanzun hannuwanta riƙe da saman kanta dake jujjaya mata. Alamun zurfi datai a tunani nason haifar mata da wani damuwan. Wani kalan zazzafan numfashi ta fesar tana hana kanta bama damar tunanin. Domin kuwa ita ɗin mutumce me tsananin taurin kai da kuma ƙarfin zuciya. Ba kowanne abu take bama yay crossed mind nata ba, Wanda kai tsaye duk ta koya hakan ne daga garesa kasancewarta renonshi ce ita ɗin. Ƙin bama ko wacce ƙofa dama tayi na zurfi a tunanin dake son bijiro mata. Knocking doorhandle ɗin da akai ne ya katse mata tunani, zuwa loƙacin jikinta har rawa yake a mugun

wahalce ta nufi doorhandle ɗin tana buɗe. Mah ce Mah ɗin ta ce dama ta sani tasan itace don kuwa bata iya kwanciya duk daren duniya se tazo taga Meesherh ɗin. Saurin rungumata Mah ɗin tay "Subhanallahi Meeshel ɗin Papiey'nta What wrong? Me ke damun ki?" Duk kuma seta bi ta ruɗe kasancewanta auta kuma ƴa mafi soyuwa a zukatan iyayen nata. Ganin duk yacce Mah ɗin tabi ta ruɗe ne ya sanya Meesherh ɗan janye jikinta ana Mah ɗin tare da ƙaƙaro murmushin dole tana furta.

"Headache ne kawai fa Maayh, Don't worry karki woni damu" ta furta wai duk a sonta na kwantarma Mah ɗin nata hankali. "A ahhh ban Isa ba wllh Meesherh dole ko dactor Asia tazo ta duba min ke" tay maganan ne kuma tana laluben number na dact ɗin, Maganan second sukai ta datse ƙiran. Kai tsaye kuma ta maida akalan ƙiran kan Billionaire Sameer Jadeens. Se dai jin ring na woyar dap da ƙofarn shigowane ya sanyata katse ƙiran, Cikin yanayi na nutsuwa da hutu da wayewa suka gama ratsawa ya sanyo kansa bedroom ɗin.

Yana sanye cikin kamilallar shiga ta blue in jallabiya ta maza se hular nan irin ta kafiye nacin nan. Zama yay a gefe da daman Meesherh ɗin suka sanyata a tsaƙiyansu. "Meke Mamana ɧaƙa?" Kai tsaye prof ***Sameer*** Jedaans ya tambayi Meesherh daidai yana kai hannunsa saman goshinta. Maganan dayay shirin yine ya tsaya may a maƙoshinsa sakamakon knocking door ɗin da akai. Umarnin shigowa kai tsaye suka bada don sun san Dr Asia jamaal ce ta ƙara so. A natsenta ta shigo har cikin bedroom ɗin, gaidasu tay cike da mutumci da girmamawa take kuma ta shiga duddubata Injection ta mata tare da ajje mata magunguna ganin ba normal damuwa bane ya sanya Dr ɗin duban su Mah tare da furta. "Don't think about it totally don't worry, the only stress paining her Ina ganin da zarar ta ɗan sama natsuwa shikenan zata warware Insha Allahu" daga haka Dr ɗin ta musu sallama ta tafi bayan sun mata godiya.Ring ɗin da woyarta a ɗauka ne ya sanya ta duba me ƙiran. Yayartace Ummetah mebin Mohan Sameer Jedaans se ita kuma data kasance autarsu, "Meesherh kince zaki ƙirani baki ƙirani ba tun ɗazun right?" Cikin muryan da yay low Sosai ta furta. "I'm sick fa Aunt"

"Subhanallahi Meeshel baki da lafiya amma baki sanar min ba?"

"No karki woni damu headache ne kawai da wata ƴar damuwa ya haifar min hakan" daga ta can ɓangaren Aunty'n nata ta furta. "Bara na barki kiyi bacci se zuwa tomorrow morning Insha Allah" daga haka suka yanke woyan tana me sake komawa jikin Mah ta kwanta abinta.Duka da kallo suke binta a loƙacin da suka gama tabbatar ma cewan tayi baccin. "Allah ya inganta min rayuwar ki Meeshel!, Allah ya dafa muku gaba ɗaya daga ke har ƴan uwanki ya kuma raba min ku daga sharrin masharranta cikin gida dana woje" tayi maganar tare da jaho hannun Meeshel ɗin ta haɗe da ƙirjinta ta rungume,prof kuwa sai wani kalan murmushi kawai yake saki. Shima jikin Mah ɗin yaɗan motsa kaɗan yana kwantar da kansa setin shoulder nata. Yana rungumeta Ya jima sosai rungume da Mah ɗin,Nan ya shiga musu addu'a shima Mah ɗin na amsawa da ameen.

Seda suka gama tabbatar ma da kansu cewan baccin yay mata nisa sosai kana suka ja mata duvet suna rufeta kana suka fita bayan Prof Sameer ya sake mata adda'an bacci.

★

The great Billionaire juraij Jedaans ne zaune kan wata ƙerarriyar cough yana snye ne cikin wata rantsatstsiyar lallausan farin yadi wanda yake lafe a farar shiny skin nashi wanda kai tsaye ke bayyanar da asalin hutu da luxurious life ɗin dayake cikinsa. Fuskansa sakaye cikin wani yankakken farin gilashi, System ce a gabansa ya zuba mata fararen idanuwansa wanda a

zahirin gaskiya bawai kallon nata yake ba ya tafi ne duniya irin ta tunani.
Wani zazzafan numfashi mara sauti ya fesar jin yanda zuciyarsa ta sake karta masa a karo na ba adadi.Yasan kaff duniya haka kuma kaff rayuwar Sheikh juraij Jedaans babu abinda yake haɗawa da bautama ubangijinsa haka kuma shi kaɗai ne abinda keda tsananin mahimmanci da girgiza dakkakiyar zuciyarsa. Me bi ma hakan baya kuma ita ce Zuciyarsa! Bugun numfashin sa *MEESHERH SAMEER JEDAANS* domin ita ɗin ta kasance tamkar renonsa ce. Duk da cewar Ƙaddara ta riga da ta buɗe tafin hannun kowannensu ta masa zanen rubutacciyar ƙaddararsa, wanda har hakan kai tsaye yay sanadiyar ban bancin ra'ayin su koma yace rabuwar su. Hakan ba shike nuna cewar ze barta har abada ba, kana hakan ba shike bayyana cewar ze barta taci gaba dayin duk kalan abinda taga dama, sosai yaji ransa ya sosu da ganin fitar Moh Saif Ameen a ɗakin nata wanda Allah ne kaɗai yasan yadda ya kwana da wani kalan masifan ɓacin ran hakan a daren jiya. Wani gauron numfashi ya kawo yana sake zubama laptop nashi farare ƙal ɗin idanuwansa.
Pisc na Meesherh yake kalla a cikin laptop ɗin idanuwansa har kalan bala'i bala'in yaji suke mai na ɓacin ran ganinta cikin wasu shegun riga da wando outpit. Wanda kai tsaye yake tabbatar da cewan a shooting film ne tayi koda ma a cikin Film ɗin ko waƙa. Ya rasa me Meesherh take nema a duniyar ta rasa dahar ta jefa kanta cikin shirin fina finan Hausa. Idan suna take da buƙatar yi ya tabbata Kaff Duniya babu inda sunan *JEDAANS POWER MENTION 💪 PEACE and RESPECT* be gama zagaya da kareɗe wa ba a duniya. Haka kuma Idan kuɗi take da buƙatar ya tabbata ita kanta tana da dukiyar da bata san iyakarta. To amma me take da buƙata a wasan Hausa?
A har kullum kwanan duniyar shine tambayar daya rasa amarya har zuwa yanzun kuwa da yake a zaune gaban System nashi. Idan kuma yay duba da yadda Ubangiji yake juya lamuransa daga kyawawa zuwa munana se ya sake jinjina lamarin ubangijin da babu kamarsa a duniya dan kuwa shine kaɗai wanda ya isa yayi abinda babu wanda ya isa juya hakan. dan yana da tabbacin idan wani na juya ƙaddarar wani da tuni ya jima da juya ƙaddarar Meesherh, A kaf cikin duniyar nan ya tabbata babu abinda ya rasa a rayuwa hakama babu abinda bazai iya zubar wa domin ganin ya dawo da Meesherh kan hanya se dai wannan maganar ta *TUN RAN GINI* da tsarin ƙaddararta ya daɗe da rubuta komai da ze wakana da rayuwar ko wanne bawa nashi. Amma duk da haka bazai gajiya ba wajen kaima Allah kukansa kan ya dawo mai da Meeshel ɗin sa hanyar daidai.
Janye fararen idanuwansa da sukai ja yayi a kan laptop ɗin a sanyaye kuma ya maida ya rufe yana sauƙe numfashi me zafin gaske. Knocking ɗin da aka danna ne ya sanya shi dawowa duka cikakken tunaninsa. "Yes Come In" cikin wannan kamilallar muryan ya bada izinin shigowa. Mohan Sameer Jedaans ne ya shigo hannunsa riƙe da wani kyakkyawan farin yaro mai tsananin kamanni da ubansa,shi kuma uban me irin kamanni ɗaya Meesherh Sameer Jadeens. A natse ya iso har inda yake Sheikh ɗin yake zaune,zama yay natse domin badan ban bancin kamanni ba da babu abinda zai hana ace uwa ɗaya uba ɗaya ne suka haife su ba. Yanayin sanyinsu iri ɗaya da yanayin shiru shiru ɗin su da kamala, wannan kamannin banbanci shi ne kaɗai ze nuna maka cewan ba uwa ɗayan ce ta haifesu ba, sedai duk da haka suna fisgen kamanni na alaƙar jini me ƙarfin da yake gudana a tsakan kaninsu.
soft Fararen hannuwansa ya miƙama yaron daya kasance me sunan shi, domin Mohan Sameer Jedaans kai tsaye sunan Sheikh juraij ɗin ya sakama yaron. Wanda Sheikh kema wani

kalan mahaukacin so na tashin hankali,Yes shi kansa yasan yana son yara sedai tayaya me zeyi auren bare har a haifar mishi yaran?
A kullum kwanan duniya shine tambayar dake addaban zuciyarsa. So da Ƙaunarsa a gun mace ɗaya yake baida feelings akan ko wacce irin macece koda kuwa zatay yawo tsirarane a gabansa. Sedai a yanzu yasan wannan ɗin ya zama kamar tarihine don ko kyauta aka bashi baya jin ze ko iya kallonta a matsayin mace, macen ma kuma ta aurensa. tun iyayensa na damuwa da rashin aurensa har suka tattara lamuran suka miƙa buƙatunsu wurin me du ka me kowa me komai wato ALLAH. Ɗan gyaran muryan da Mohan yay a karo na biyu ne ya dawo dashi daidai ɗin sa. Magana ne sukai akan zaman meeting ɗin da yake da shi da ƙarfe 11:30 na yau. Daganan suka ɗan tattauna maganganu akan yadda al'amuran kasuwancin nasu yake tafiya.

★Araund 7:50 kowa na gidan ya gama kammala kansa a babban dining room na gidan inda room ɗin yake ɗauke da rassa daban daban na dining table. Meesherh itane ƙarshen fitowa kuma dama kusan kullum itane last, zama tafi fuskan nan ta kan daren jiya kan wayewar yau ta sake yin fiyau. Bata ɗaga kanta ta kalla kowa ba bare ma woni yay tunanin kawo mata wargi, kamar kuma yadda bata gaida kowa dake room ɗin ba.
Annie ce ta dubeta cike da jin zafin da bata san kona miye ba ta furta. "To Ishashshiya tunda babu tarbiyyar girmama na gaba dakai se a tashi ayi saving namu dinner,Mutum kuma in yaji haushi ya ajje aikin shirmen da yake ya koma Islamiyya kodan sanin yadda ake girman na gaba dakai"
Idan ƙasar dake wurin tayi motsi to kuwa tabbas Meesherh ɗin ta yi itama. Don haka wurin ya ɗauka wani kalan mugun shiru kowa na kissima abubuwa maban banta a cikin rayukansu. Papiey' ne kawai yay ƙarfin halin duban inda Meesher'n take bawai don beji zafin maganan da annien tay akan gudan jinin nasa ba. A ahhh sedai kara da kawaicin da ya saba ma yayyensa iyayen su juraij ɗin kenan. kasancewar shi autan su kuma mutum mafi haƙuri da jure ko wanne kalan ƙalubale daga Ahalin nasu. Ɗan zafawa yay tare da furta.
"Mamana bata ji ana magana ba ne?" Prof Sameer Jadeens yay maganan yana duban inda Meesherh ke zaune. Cike da rashin haƙurin da mijinta Sameer Jadeens yaga ta kowa take dubansa, domin kuwa ita ɗin ba sakar ya bace da zata ji ana muzanta jinin ta kuma tai shiru, "Amma ai Papiey'n Meeshel kadai fi kowa sanin cewan Meesherh bata da lafiya? Ko duk ba gasu Nainerh nan ba, su Aysha su Nanameerah su Salma ba se ita kaɗai za'a kalla ace tayi saving namu dinner"
Ya buɗe baki kenan da nufin mata magana Jedaans turaki ya katse shi ta hanyar masa nuni da eat kawai don wannan loƙacin dinner nasu ne. Kafin kowa ya miƙe Annie ta miƙe ranta na mata suyar ƙin tanka tan da Meesherh tayi. Hakan ya sanya cike da fusata ta furta, "A dai koma Islamiyya ko a samu rabon kusanta kai ga Allah"
wani irin shiru mai saka duk wanda ya shiga mutuwar jiki gurin ya ɗauka, Don hatta metres sarvice ɗin dake ta aikin kai da koma a wajen tsit sukai.Kallo ɗaya Maminsu Moh Saif Ameen tama ma'aikatan wurin suka tare duka a take.
Ajiyar zuciya me ɗan ɗumi Sheikh ya sauƙe a natse, se kuma ya miƙe tsammm a wurin se dayay taku ɗaya ana biyun a dakata. Cikin wannan natsatstsen low tong voice nashi ya furta.
"Kiyi haƙuri Annie Amma kai tsaye daga yau na soke duk wata magana da zata fito daga

bakin ki akan baby da Mah, Indai bame daɗi bace kai tsaye da yawun bakin Abbie nay magana" daga hakan ya sanya kansa yana barin room ɗin baki ɗaya, yanajin hankalinsa na dawowa jikinsa kodan umarnin abbiensa daya cika akan annie'nsa.
ɗago idanuwanta rinannu tai da sukai laushi ta kalla Eng Thabit Jedaans wanda shima juyowa yayi ya kalleta da idanuwansa da suka nuna babu wasa ko wargi a cikinsa.wata bahaguwar ijiyar zuciya ta sauƙe ahankali tana matse hannuwanta duka biyu a wuri guda.Ga Wani kalan shegen sanyin da taji yana ratsa ilaihir gangar jikinta. Wani kyakykyawan murmushi tsohon ya saki wanda ya fito da ƙananun teeth nashi farare tasss kamar ba na tsoho ba. Kai tsaye zaratan magidan tan ƴaƴan nashi suka bishi da ido. Wani murmushin ya sakar musu na badai zaku fahimtar komai ba. Daga haka ya miƙe tsaye da ƴar sandarsa ta narkakken zinare me sheƙi yana barin parlour'n baki ɗaya ma. Daga haka suma kowa ya miƙe kasancewar sun san lalle kenan akwai abinda tsohon yake shirin aikata koma yana dap da aikatawar.

*Sheikh juraij*

Kai tsaye katafaren dogon ginin sa ya nufa ba hasalin wanda yake a ciki yanzun ba. A cikin can ƙasan zuciyarsa yake furta. "Hamdan,khathiran,ɗayyuban barrakhallahufihi!!!" Domin ma ya rasa abin magana akan Anniensa ya kuma rasa wanda kalan tunanin ya kamata yayi. Nosemask ɗin dake cikin aljihun farin dogon yaɗin jikinsa ya ɗauko yana sakayawa a face nashi.
duk rabin face nashi a rufe da nose mask ɗin se glass ɗin daya sanya. Amma hakan ba shi ne zai hana ka gane cewan shi ɗin kyakkyawa ne ajin farko ba, Yana da murɗaɗen jiki haɗi da murjewan fata,yana da wani irin faffaɗan ƙirji tamkar irin India actor's ɗin nan.Damtsen hannun san nan tamkar sa fashe saboda training gym da yake yi a ko wacce safiyar duniya.
duk girman wajen shiru babu motsin ko wanne rai me numfashi, dama haka yake sau da dama yakan zo sa'i zuwa sa'i don kaɗaita kansa daga kowa musamman idan yana hali na damuwa.zaune yakai kan wata fara tas ɗin sofa. jikin nan nasa se glowing na ƙyau da kyau kawai yake kai ka rantse da Allah bai taɓa taka koda ƙasa bane, Saboda tsananin laushinta da kuma yadda take ɗaukan ido na tsantsan kyau. Gashin nan a kwance luff luff tamkar wani renon larabawa ko turawa.Duk inda kaji an ce Sheikh juraij thabit Jedaans to ana nufin wannan Kyakkyawan farin matashin malamin ne mai jini a jika, sosai yake da hasken fata da kallo ɗaya mutane suke bashi sunan ***Bature*** ko ***Balarabe***.
dogone cikakken namiji me cikqkkan wayewa na addinin Islama daya gama ratsa jinanen jikinsa, yana da faffaɗan ƙirji wanda yasa kai tsaye muscles nashi bayyanuwa sosai. Wannan kyakykyawar Innocent face ɗin nashi ɗauke take da dogon hancin da ya ƙara wa fuskarsa wani kalan kyau da zati, ɗan karamin bakinsa ɗauke yake da kyakkyawan Pink lips kalan masu shining ɗin nan tamkar wanda ake goga musu lipstick. Wanda hakan ba ƙaramin kyau ya ma ɗan ƙaramin bakinsa ba ta hanyar masa ƙawanya.
A hankali ya ɗago da dara daran fararen idanuwansa masu kama da ana musu ɗuren madara masu shegen kyau kamar yasa musu ƙyalli, kwayar idanuwansa da ta kasance light irin me tsananin hasken nan mai ɗaukar ido, idan kayiwa idon na shi kallo a fusge sai kaga kamar ruwane suka tarun masa a cikin eyes ɗin nashi. Don kuwa sedai a fisgen don da matuƙar wuya kace ka taɓa iya haɗa ido dashi koda na tsawon 1 mints ne. Don wani irin kwrjinine dashi

Daga haka ta nufo ƙasa ta sauƙo kamar yadda ta zata duk iyayentan suna babban parlour'n gidan ne. Tun kamin ta iso wannan shegen ƙamshin tan nan ya gama sanar musu cewar me zuciyar ~~jedaans~~ ce gaba ɗaya ke tafe wato ***DIAMON*** MEESHER ***Sameer*** JEDAANs. Daga gefen Mah ta zauna bayan ta gaida kowa dake dining room ɗin. plate ɗin dake ɗauke da donut, pizza se picanto taja gabanta tare da ɗauka tana ɗora shi kan cinyarta tare. Metres sarvice ɗin dake aikin shirya kitchen Meesherh ta kwalama ƙira tana bata umarnin kawo mata fruits. Babu

jimawa kuwa se gata hannunta riƙe da plate da yankakkun fruits ɗin a ciki masu sanyi, da akama yanka ƙananu².

Nanameerah ce ta ɗan kalla inda Meesherh ke zaune ƙanwa Moh Ameern Saif ta furta wallh Aunty Meesherh kalan yadda kike gudanar da acting naki wurin aikin ku na burgeni wllh" Ɗan murmushi me faɗi tay tana kallon Nanameerah'n itama tare da furta. "Sosai mutane ke faɗin wllh aikin mu film na burgesu sosaifa Nanameerah" a tare kuma suka saki murmushi wa junan su cike da shaƙuwa. Annie ce ta kalla sashin da Meesherh ɗin take tare da furta. "Aikin me? Ke yanzu har wani abun kirki da alfahari kika ɗauki sana'ar taki, Ko da yake aifa aikin tallata jiki a yanzun kam shine babbar sana'a a Nigeria"

A rene cikin wani ɗan iskan renin wayo da rainin hankali ba tare data ko kalla inda Annien take ba ta furta "Nagode!"

Tsaye ta miƙe da niyar barin dining room ɗin. Abba ne ya kalleta da alamun damuwa a ranshi ya furta.

"Mamana ina kuma zaki bayan baki ko kammala yin dinner naki ba?"

Shafafen cikinta da ba kamar yanzu ta gama cin donut da pizza haɗi da picanto ba sam kai ba kace ma kwai ƴaƴan hanji a cikin cikin nata ba. Ɗan shafa cikin nata tay tare da furta.

"Alhamdulilah na ƙoshi ne Abba"

"Ok shikenan Mamana Ubangiji yay Miki Albarka, da ameen ta amsa bayan ta sake musu sallama don yau tana da wani shooting film da za'a ɗauka wanda Film ɗin tane itane da kanta ta tsara abinta.Har taje bakin ƙofar parlour'n kamar daga sama ta tsinkayi muryawan Ama tana me furta. "Takwarata taimaka ki sauƙe min yayanku a gidan gwaggo Haleemah"

Cike da ɓacin Ran daya kasa dannuwa Annie ke kallon Ama data kasance surukuwa a gare su kafin cikin hucin ɓacin rai ta furta

"Haba ama bayan batama zuri'armu suna da tay, duk hakan be isheku ba sema ƙoƙarin dan gan tata da Mutum tsarkakakke kamar juraij da kuke! Don me ake min haka ne eye? Kodan kawai kina matsayin Yaya ga Mahaifiyata? To ni wllh na gaji nima kawai daga yau ki dawo yimin kallon surukuwarki ba ƴar ki b......

"Zeynab!!!"

Abba ya wani irin ƙira sunanta a mugun tsawacen da ya sanya kowa rawan jiki a wurin. Don ba abu bane daya taɓa faruwa a zahirance duk kuwa irin tijara da jalalar da Annie'n keyi akan duk wani abu daya danganci Meesherh ɗin. I'm sorry Abban jur..."

Ta furta muryan ta na rawa.

"I said get out my friend!"

ya sake buga mata wata uwar tsawar da tafi ta farko ba shiri ta haɗiye maganar da bata ƙarasa taba tana barin wurin don A yadda ta ji muryarsa a kausashe kam ta tabbata babu wasa a cikinta.

Jiki a sanyaye kowa ya shiga darewa banda Mah da jikinta har wani jijjiga jijjigan ɓacin rai da baƙin cike take yi, Sa'ar ta ɗaya sunan ALLAH ne ya fara zuwa bakinta kafin komi shi yasa ta dinga nanata sunayen ALLAH'n a bakinta.

Meesherh kuwa tana fitowa compound na gidan ta tsaya tare da ɗan sa hannunta na dama

tana riƙe ƙugunta. Nainarh ce tsaye ƙaramar autarsu Sheikh juraij jingine da jikin motar ta. Wani irin kallo Nainerh take watsama Meesher'n tare da furta. "Har ke wa ce ce a cikin gidan nan da har zaki ringa mahaifana meda yawu akan ki gaban mutane?"

Wani kalan sheƙeƙe Meesherh ta mata "Kin ga kenan ke da kanki kin ba kanki cikakkiyar amsarn cewa Ni ɗin wata aba ce me girma a cikin gidan nan, Idan kin gama bani hanya ta zan wuce"

Tay maganar tana kama murfin car nata tana ɗora haɓarta akai, ta buɗe baki kenan da nufin sake watsoma Meesherh ɗin wata rashin kunyar idanunta ya sauƙa akan babban yaya wato Sheikh juraij thabit Jedaans. Babu shiri ta gimtse bakinta tana haɗiye sauran maganar data saura a cikin bakinta. Tamkar kiftar ido haka Nainerh ta ɓace a wurin. Zuciyanta a cunkushe ta shige Motan tana zama mazaunin Driver yayin da ya zauna gefen mai zaman banza. A natse tasa hannunta farare ta kunna motar cikin yanayin nutsuwa take driving nata, Yayin da shi kuma yake gefenta zaune. Ahankali yake ƙarema zara-zaran yatsun hannunta dake kan stearing tana juyawa kallo,me kama da kalan nashi don sosai abubuwan su suke ɗibar kamanni harta da sawayenta kalan nashi ne futiƙ,wani ɗan numfashi ya fesar tare da furta.
"Bani motar nan b.... Ji yay ya tsinta kansa da kasa ƙarasa sunan Babyn da yay niyar faɗi.Se ma lumshe idanunsa dayay tare da shaƙan ƙamshin humranta daya cika motar. Ita kuwa bata kawo komi a ranta ba sema kallon yanda ya lumshe idanunsa tay se taga ba ƙaramin kyau ya mata ba. A jikinsa yaji kallonsa take se kawai ya gyara fuskan da kyau yana jingina kansa da jikin motar, Kamar kuma ba zai yi magana ba buɗe lips inshi a hankali yay tare da furta. "Kallon fa?"

Kanta ta ɗauke wani munafikin murmushi ɗauke saman fuskanta. "Pa'apahh!!!" Ta ƙira hasalin ainihin cikakken sunan shi gareta tun yarinta.Hakan ne ya sanya Idanunsa dake lumshe ya shiga motsasu ahankali yana son buɗe su tare da faɗin. "Buddies kiyi abinda ke gabanki, ko kiban motan!"
Buɗe idon ta da yanzu ne ta lumshe su dama tare da juyowa ta kalli inda yake zaune, iyaka muryansa kaɗai da taji ya sauƙar mata da samun nutsuwa. "Pa'apahh to kace ka yafe min pls" tay maganan da alamun rauni sosai tattare da ita. "Da ki kamin me kenan fa?" Yay maganan cikin ko in kula. "Everything forget itt" Kansa ya dauke a kallonta yana maida shi can kusa da closed windown motar, Itama se bata sake furta komai ba don tasan bayi son maganar kenan.Nuvel script ɗin ta dake gefe ta ciro me ɗauke da photon'nta tana budewa ta ɗaura shi saman gaban motar. A duka sassan jikinsa ya soma jin banbancin yanayi.
Sake buɗe idanunsa calmly akanta yay, wacce ta nutsu wurin driving nata a kuma daidai loƙacin suka kawo ƙofar get na wani makeken ƙaton get. nitsatsassun fararen idanuwan ta da suke nan sakk nashi kawai ta zuba akansa. tamkar wacce bata da wata matsala a rayuwarta tamkar babu abinda ke damun zuciyarta ta furta. "Pa'ap.... Bai bata wani dama na ƙara sa ambatar sunan shi da tay shirin yiba ya fi ce a motar. Wani irin shiru tay tana me binsa da kallo da raunatattun idanunta. dan Shiru tayi na wani loƙaci kana taja kan motar ta tay reverse tana shan kwanar da zata bi. Cikin son shanye komi cike da nitsuwa take ci gaba da tafiyanta kamar daga sama taga wata babbar mota tayo kanta. Tamkar wacce aka bugama guduma haka taji amon muryansa cikin wani shuɗaɗɗen lamari yana furta "Babyyyyyy.....

A wani irin tsiyace ta taka wani mahaukacin birki tare da juya kan motar ta zuwa ɓangaren gabas, wannan babbar motar da tayo kanta na bugar wata motar daban ba ita ba.

★★

Slowly ta shiga buɗe idanunta da taji sun  mata nauyi loƙaci guda, ɗan lumshesu ta sake yi tana ƙoƙarin saita kanta dan koda wasa batai tunanin  zerewa motar ba. Wata ƙatuwar Ajiyar zuciya ta sauƙe me nauyi. Tana ambatar sunan ALLAH cikin rai da ruhinta.  ★ Ɓangaren Sheikh juraij kuwa a natse ya sanya kansa cikin ƙaton parlour'n gidan, da gwaggo Haleemah wacce ta kasance kaka a gareshi ya fara cin karo. Gwaggo Haleemah yaya ce ga Ama kuma ita kaɗai take da ita ƴar uwa anan kusa idan ka cire dangin su dake saudia. "Aaaahhh lale marabu da babban angona, Juraij yau kuma kaine da kanka?, Kodai ɓatan hanya kayi Ni Ko nace banda wajen zaman masu ɓatan hanyar?" Tay maganar da murmushi kwance saman fuskarta. Zama yay daga saman 1str ɗin dake kusanta. Zamansa babu daɗewa kamar an cillota Samha ta shigo cikin parlour'n zaram tamkar ana tunkuɗota.

Samha ƴa ce ga Surayya  ƙanwa ga Annie kenan wacce kuma suke ƙoƙarin haɗa aurentane kuma da juraij ɗin, sedai sam yarinyan bata da kamun kai amma su basa ganin hakan babban burinsu kawai auren ya haɗu. Se data ta shigo kuma cikin mugun bariki da kisisina ta wani sinne kanta ƙasa tana furta. "Laaaah dama uncle kaine? To sannu da zuwa Bara a kawo maka juice" da hannu ya mata halaman bai buƙata. Dan faɗa fuska tayi tare da duban gwaggo Haleemah tana furta, "Gaskiya gwaggo ki ma Uncle juh magana! Shikenan yazo shi kullum ba zai ci abincin mu ba inda Ni ce na ce zan kawo mishi"

Dan murmushi irin nasu na manya gwaggo Haleemah ta yi tana furta "Yo in banda abin kima Samha kwana nawa ya rage miki, ku ce kan kita masa girkin kalan wanda yake so, kuma dai kinsan juraij bai fiye son komai a sake ba, amma idan da gake se shi ne seki ta lallaɓa kayanki ko" ta ƙarishe maganan da Murmushin nan ɗauke saman fuskarta. Dariya ta saki tana rufe idonta wai ita ala nan dole an bata kunya.Daga haka ta shige dayan parlour'n dake kusa da wannan ɗin shi kuwa a natse yaja fruits ɗin dake gaban gwaggo'n apple ya ɗauka ya ɗan ci kaɗan. Bayan bata saƙon da yay ya miƙe da shirin tafiya. Suraj ne ya shigo parlour'n da yake shima jika ne ga gwaggo Haleemah'n. Gefensa ɗan wani matashin saurayi ne suna tafe gwanin birgewa.  "Ahhhh yau wa nake gani kamar babban malami" ya fadi a washe hakwaronsa farare tasss waje, Bai bi ta kan iya shegen da suraj ɗin ya soma mashi ba yana bama matashin hannun suyi masabaha.  Don ya san idan ya biye ma suraj ɗin babu ruwansa kunya ne kawai ze bashi.

Ita kuwa gwaggo Haleemah bin bayan Samha tay, zama tay gefenta  suka soma fira cikin dabara gwaggo take dan son lurar da Samha'n kan lamarin Sheikh juraij ɗin da ake shirin  aura masa dap. Sedai maganan bawai tama ko fita bane iyaka yasu ya sune suke ƙusƙus dinsu tsakani. Sosai firan da gwaggo take mata akan juraij ɗin ke mata daɗi da sanyata nishaɗi

♡

Rasss gabanta ya mugun buga mata don ganin drector Muhsin Aliey Yahaya tsaye da wasu yara wanda kana kallon su kwanyarka zata Hasko  maka cewan ƴan daba ne. Sedai shanye tsoron nata bayyanuwa tay tana karasa fitowa a motar nata kai tsaye ba tare data kalla inda yake ba ta shigewanta inda zasu gabatar da shooting film ɗin ta na. ★TAURARUWA♡

Film ne da take son yin cleaning up nashi Kan yadda waɗanda taurarinsa suke Haskawa a cikin duniyar suke wulaƙanta mabiya dama masoyansa. Tana shiga hall ɗin Hotels din da za'a gudanar da shot ɗin suka dauki sowa da ihun ƙiran sunanta.

Kanta ta ɗauke daga kallon Moh Ameern Saif daya kafeta da ido. Nan aka soma gudanar da shirin cike da birgewa.

Ba itane ta sama kanta ba se wajajen 5:40 pm. A matuƙar gajiye lilis ta fito daga cikin hall ɗin tana jin matuƙar haushin kanta na kin tahowa da ko gurds ɗaya da batay ba. Jingina da jikin Railer'n dake gaban hall ɗin tay idanunta lumshe. Ko dinner gaza yi tayi haka har wata actress me suna Khadija Yobe ta fito itama ta sameta.

"Meesherh lafiyan ki kuwa?"

"Hummm kedai Khadijah kyaleni wllh duk a gajiye nake jima nake kamar bazan iya driving ɗin nan bane ma wllh"

"Me zai hana idan har babu damuwa na miƙaki gidan" ɗan numfashi ta fesar tana furta "No ba ma se kin hawal da kanki ba na kira ayrah amoh nace ta biyo ta nan ta tafi dani"

"Kuma kina ganin har loƙaci bazai ƙure miki ba kanta ƙara so?" Khadijah yoben ta tambaye ta ko kafin ma ta bata amsar sega wata arniyar farar Roy *R* Rayce nan na danno Kanta cikin Hotels ɗin.

Har gab dasu motar ta ƙaraso kafin a natse aka soma yin kasa da glass na motar, wani kalan zaro fararen idanuwanta woje tay don ganin..............

To ai Shikenan muma semu gimtse 👌

*BY AMMEY LAYLERH*

Chat mee view
My phone
07085041758
Or
08104493215

Don son magana dani AMMEY LAYLERH chart Mee or call a wannan No ɗin 08104493215

Masu neman *MIKIYA* ma har yanzun ƙofarku a buɗe take har yanzu yana nan akan farashin sa na ₦ 500 ban ƙara ba kamar yacce na ce a baya.

https://whatsapp.com/channel/0029Vb4EHwq6LwHgpTokZA3D

⌣ஐ⌣

*⌣ஐ♡𝕋𝔸 ***DA***𝔹𝔸***N***☆ஐ⌣*

_𝓢p̶eci̷ɑʟ _
♡
***Maryam Naseer*** ɱi̷ɾɾɑh

***_AMMEY LAYLERH_***

***Page***

9&10

✯ *🌠 JAJIRTATTU WRITER'S ASSOCIATION💫*
(J.W.A)

https://www.facebook.com/61556643936657/posts/122103978398221464/?substory_index=1596987511055341&mibextid=rS40aB7S9Ucbxw6v

_Rubutu baiwa ce daga Allah, jajirtattu ne kawai kan iya amfani da wannan ƙasaitacciyar baiwa su sauya tunanin al'umma cikin sauƙi_.✏️*

****I DEDICATED TO GOVERNMENT GIRL UNITY SECONDARY SCHOOL MALAM MADORI PMB*** 001*

♡♡♡♡♡♡♡♡♡♡♡

Don ganin Papiey'nta da tai zaune cikin car ɗin, duk da cewan ba abin mamaki bane a wurinta amma na yau ɗin se ya fi koda yaushe bata mamaki. Wata kyakykyawar ajiyar zuciya ta sauƙe me ɗan ƙarfi tare da nufo car ɗin ita da jaruma Khadijah yobe. Itane ta buɗe mata gaban motar kusa da Papiey'nta ta, car key nata ta miƙa mata bayan ta gaida Papiey'n tare da cewa tayo dropping car ɗin zuwa gidan su tun da dama ba sa da woni tazara sosai. Itama Khadijah yobe ƴar masu hannu da maiƙo ce sedai idan dasu Meesherh Jedaans a wuri babu Powerful ɗin kowa da ke aiki a kafff ma faɗin garin Kd da zagayenta.

"Papiey yau ka tuna dani kenan?" Shi ne tambayar data fara jefa ma mahaifin nata Duk da tasan cewan tasan kwanan zancen ba zai wuce sake kwantar mata da zuciya da zai yi ba. Left hand nashi da baya driving dashi ya sanya yana kama nata tafin tare da jimƙewa a cikin nashi,

cikin tsananin jarumta da ƙarfin hali da kuma son kwantar mata da hankali ya furta. "Baby ita Rayuwa da kike kallo komai yana zuwarma bawa ne ga bisa umarnin abinda ya tsara a cikin tarin Rayuwarka! Ina son kici gaba da shanye komai da zakici gaba da fuskanta daga can gida, amma ba ta yadda komai ɗin ze zama illa wa taki Rayuwar ba. Insha Allah wannan karan komai ya kusa daidaita da yardan me du ka wato Ilahu Sarki ALLAH, Sarkin da babu kamarsa buwayi gagara misali ina..jin... Ina...jin...ina.........jin matuƙar ciwo sosai da ɗaci kan aibantamin MY BABY'n Papiey da ake...

Muryan shi ce ta soma rawa da ƙoƙarin karyewa dan haka yay shiru yana sake damqe hannuwan Meesherh ɗin da ɗan ƙarfi yana qasa da idanuwansa da suke neman cikowa da hawaye. Don sosai Maganan Anniey ya buge shi se dai samm baya taɓa damuwan komi akan face nashi kan duk wani mahluki dake cikin estate ɗin nasu koma na ce family.

Jin rauni ya wanzu a cikin muryan papiey ne ya sanya ta itama ɗin sake kame hannuwansa cikin nata ta na kasa cewa komai dan tasan kuma ba zai iya ci gaba da maganan ba kenan.

Ɗan lumshe fararen idanuwanta tayi A bayyane kuma ta shiga furta adda'ar "Rabbi inni lima anzalta ilayya min khairin faƙir³ Ra rabbi inni magalubun fantasir³ la haula wala quwwati illa billahil aliyal azeem³, Innalillahi wa'inna ilaihi raji'un ³" haka ta shiga ambata tare da sauran adda'o'in da duk suka zo cikin bakinta. Ajiyar zuciya me sanyi papiey ɗin ya sauƙe a natse yanajin hankalinsa na dawowa jikinsa take yaji dacin zuciyarsa ya ragu sbd yadda adda'o'in data karanto ɗin suka ratsa shi sosai tare da zuciyarsa.

slowly kuma ta shiga ware idanunta tare da sake sanya hannunta tana jinginar da kanta jikin papiey ɗin nata, daga haka tafiyan nasu ya koma na kurame har suka ƙara so mahaukacin estate ɗin su, Shi ya fara fita jikinsa duk a wani kalan amma yadda yake tafiyan cikin nutsuwa kai kace babu abinda ke damun Rayuwar sa nan. Lugagge bag na papiey kawai ta dauke se handbag nata tana bin bayan mahaifin nata. tana tafiyar ne kuma tana ɗan shedding tears nata zuciyan ta na ƙara yin nauyin abubuwa da yawa da suka kanainaye cikin rayuwarta.

A bakin entry na babban parlour'n gidan sukayi kiciɓus da Moh Ameern Saif inda ita ta tura shi kuma ya turo. Kin sakin ƙofan tayi tana kuma ƙin kallonsa, sake murɗa handle door ɗin yay yana jan ƙofar baya ya kuma ja ya tsaye yana ƙare mata kallo tun daga samanta zuwa ƙasa. A ɗan kausashe ta furta "Moh Bani hanya"

Ɗan girgiza kai yayi kawai tare da ɗan taunar lisp nashi, Wani shegen killer smile yayi tare da ɗan shafar gashin ƙeyarsa yana me furta "Ohh Ohhh beb wai cikin sauƙi haka?" Yay tambayan cikin ɗan iskan salon jan hankali da kuma rashin mutumci. Chakkk ta tsaya daga ƙoƙarin raɓa gefen Moh Ameern ɗin da take niyar yi. Sakamakon tausasan hannuwan da taji ya raba tsakanin su ta hanyar janye ta daga niyar shigan, ko bata juyo ba ZUCIYAR TA ta riga da ta gama sanar mata ko wa ne ne. Hakan yasa ta jan idanunta ta lumshe su gaba ɗaya. Moh Ameern daya ƙame cike da tsoro da kuma kafe Sheikh juraij ɗin da ido yake kallonsa, Shima idanuwansa da suke a rufen ya buɗe tarrr akan Moh Ameern. Kafin ya saki wani murmushin rainin wayo tare da zamar da ƙasan lips nashi ya furta. "Shi kuma wannan ko a cikin wanne hadisin ne ko sura ohooooo, amma ko ba komi abin ya bada gitta da ƙyau Sheikh babban salo!!!"

Haka muryan juraij ɗin ya dake shi Sheikh juraij ɗin. A natse ba tare da garajen komi ba ya rabata da jikinsa yana jefawa Moh Ameern ɗin wani kalan mugun kallo me tattare da cikakken gargaɗi. Ita ne ta fara barin wurin tana jin yadda ƙirjinta ya ɗan ƙare mata tare da mata wani

kalan nauyi wanda dama har yanzun bawai ta gama warkewa bane rass.

★A ƙaton parlour'n su wanda yake ɗauke da duk wani nau'in jin daɗin rayuwa ta tarar da duka su Maamah har dama ƙarin babbar yayarsu ummeterh. Da sauri ummeterh ta nufo ta tare da riƙe hannunta fuskanta ɗauke da kyakykyawan Murmushin da ya sake fidda tsananin kamanninsu kasancewar su duka Ukun kamanninsu ɗaya. "Ma sha ALLAH Dear lallai jiki yayi sauƙi tunda har aka iya fita shooting yau" ɗan murmushin yaƙe tayi tana shafa kan baby'n nuwaira da ita ma ta nufo su fuskanta cike da farin cikin ganin Aunty Meesherh ɗin. "Dama ay duk laifin Maamah ne banda haka ai naji sauƙin sosai!" Maama'n da itama ta taso daga idda take zaune ne ta dawo ɗayan gefen Meesherh'n ta zauna ahankali tare da dafata fuskan ta da ɗan murmushi ta furta "Ko yanzu nasan babay'n papah ba ta da cikakken lafiya kawai dai kina danne hakan ne na sani"

"To banda abinki Mamman'su Karfa ki manta Meesherh fa ita ma ce ce wata rana haihuwa zatay, tun daga yanxun idan bata koyi ƙarfin hali ba se yaushe kike son ta koya?" Papah ya bata amsa da hakan yana hayewansa sama. Mohan Sameer da shigowansa kenan parlour'n shima yama kansa mazauni akan ɗaya daga cikin expensive chairs da suka ma parlour'n ƙawanya. Yana ɗora ƙafarsa ɗaya kan ɗaya yana fuskantansu su duka cike da farin cikin ganinsu su dukansu. Aunty Ummeterh ya fara gaisarwa kana ya sake gaida Maamah duk da kuwa cewan babu jimawa suka Hausa ɗin. Lil juraij dake riƙe da hannun Mohan ɗin ne ya zame cikin wayonsu irin na yara kai tsaye ya nufi inda Meesherh take, duk kuwa da yadda take ƙoƙarin ɗauke fuska daga yaron,cikin muryan gyaranci ba sosai ba ya ce "Otty kin ga ni paap ne ya bani kuma yace karna fatawa kowa ma" yay maganan cikin gwaranci ba sosai yana mata nuna da wani Rolex watch na diamond gold me kyau kalan na yaran nan me shegen tsada da kyau. Ɗan taɓe baki Maamah tayi tana juyar da kanta daga kallon yaron tana maidawa kansu Ummeterh da Mohan da suke wata maganar daban.

Miƙewa tayi da niyar tafiya amma lil juraij ya maƙale mata duk yacce ta so data yagar dashi kuwa. Gashi zuwa loƙacin kanta sosai taji yana juya mata gashi wasu masallatan harsun fara ƙiran sallah, dole dashi ta tafi sama yana maƙale da ita. Duk da ido suka bita kafin Mohan ya kalla Maamah tare da furta "Maamah don ALLAH Meesherh ta dakata da aikin nata don yanzu kamata yay ace tana gidan aurenta, Ki duba fa tana age na 24 year's ba ai yaci ace ma tana da nata babay'n itama" tunda ya soma maganar Maamah ta kafe shi da ido ko ƙiftawa batayi seda ta tabbar da ya gama ta furta.

"To sannu ubana da wannan ai kamata kawai yay ka bani umarni, ka ga Mohan ka fita ido na In rufe idan har kaima ba zaka iya bin Meesherh da fatan Alkhairi ba to kamata yayi kaima ka janye idanuwanka daga gare ta" ta ƙarasa maganan a fusace tana miƙewa tare da barin parlour'n baki ɗaya, don Maamah irin iyayen nan ne masu shegen S0n ƴaƴansu wanda basu ganin laifinsu ko kaɗan, se dai sammm bata barin ko waye daga cikin yaran nata ya aikata ba daidai ba kuma ita mutum ce da bata iya ƙunbiya ƙunbiya da abu ba ita ɗin karan tsaye ce ƴar kai tsaye me gaɓa². Ko waye ya taka ta to kuwa lallai itama zata taka shi don bata ɗaukar raini kamar yacce itama bata raina kowa se har in mutum shi ne ya fara shiga hurumin ta da wata sigar ta daban, to kuwa lallai anan ne zaka gane ko kai ɗin wane ne.

Ajiyar zuciya me tattare da damuwa Ummeterh da Mohan Sameer suka sauƙe kusan loƙaci guda kan kalaman mahaifiyar nasu, duk kuwa da cewan ba yau bane suka saba fuskantar hakan daga gareta. kawai abinda suka sani suke kuma so shi ne suga sun inganta rayuwar

Autar nasu, sun gaji da ce ce kucen da ake akan Meesherh ɗin daga media harma da nan cikin gidan nasu kuwa. Tabbas hakan na masu ciwo da kuma matuƙar ƙona musu zuciya.

†

*Sheikh juraij*

Tunda yabar wurin kai tsaye cikin garden yay shigewansa, sanyi da kuma iskan dake kaɗawa a wurin na ratsashi wanda har yake jin kamar fatar jikinsa ce ta bude kai tsaye sanyin yake ratsa masa ko wanne sassa na jikinshi yana daskarar da duk wata magudanar jini ta jikinsa, kamar kullum yana sanye cikin shigar farin yadi me azabar laushi da tsada ɗinkin jumper cables irin na zamanin nan amma kuma ba masu sherp da yawa ba irin na matasan yanzu. Sumar nan tasha gyara na musamman se fidda daɗdan ƙamshin take yi gami da daukar ido. Sajen nan yay luf luf abunsa har wani kalan shine blue yake bayarwa daga nesa.

Sanyi haɗi da daɗin iskar ne ya sanya shi kasa zama wuri guda don haka ya shiga zagaye cikin garden ɗin,Hannuwansa goye a bayansa daga can ƙasan zuciyarsa kuwa yake furta.

_Subhanallah,wal hamdu lillah, wala'ila ha ilallahu wallahu akhbar³_

Da dai duk sauran adda'o'in da duk suka zo bakinsa, kai tsaye ba zaka taɓa fuskantan tasbihi yake ba sedai ka kalla fatar lips nashi kaɗan tana motsawa. Sammm yama rigada ya manta da abinda ya farun yanzu ko na ce dazu. Ganin loƙacin ƙiran sallah yayi ne ya sanya shi fita, se da ya fara shiga bedroom nashi kana ya fito kai tsaye yana shigewa cikin babban masallacin dake cikin anguwarsu. Shi ne ya ƙira sallar ya kuma ja jami'i cikin wannan daddaɗan sautin nashi da sauraran yanda yake fidda tajweed nashi yake sanya mutane cika masallacin duk kuwa kalan girman da yake da.

Dama shi ka'idan sane baya shigowa se bayan sallar Isha'i sosai shi yasa kowa na gidan ke riga shi kammaluwa a dining room ɗin,duk da kasancewar tonight baya zaman dining room ɗin amma kuma hakan jiran shigowarn nashi ya zama kamar al'adan kowa.

Iyayensu mata kawai ya gaida kasancewar sun gaisa da iyayensu maza tun a can cikin masjid ɗin.Nan ƙannashi maza da matan suka gaida shi shima,A natsensa ya amsa su yana kallar bakin Meesherh da kuma Moh Ameern Saif da babu su a cikin jadawalin gaisuwar.

Directly balcony ɗin da ya saba zama kai tsaye wuce maids ɗin dake aikin shirya dinner ɗin na binsa da tea plask ɗin dake ɗauke da zazzafan tea wanda duk daren duniya shi ne kawai yake sha. Jere mishi tay daga inda yake idanunsa lumshe yana ambatar sunan ALLAH acan ƙasan ranshi. Se da ya tabbatar ta bar wurin kana ya buɗe idon yana jan tea plask gabansa. A natse yake sipping tea ɗin abinsa daga gefe dashi kuma System nashi ce yake aikin sarrafa ta. Yau be daɗe a wurin ba kamar kullum ya tashi ya tafi don yana da abinda zeyi a daren. Ga yawan bugun da zuciyarsa ke mai akai akai yana jin tamkar wani abu mara daɗi na dab da faruwa dashi, Amma sosai yay ƙoƙarin danne hakan se adda'o'in sa da yaci gaba dayi yana adda'an koma miye zai faru dashi to Ubangiji ya kawo shi cikin sauki ya kuma takai ta ma masa ɗin, da haka yanar wurin yana daura alwula tare da fara jero nafil fili wa mahalicci'nsa...

☆ Meesherh kuwa koda ta koma bedroom nata wanka tayo ta shirya kanta cikin singlet ta mata da wando. Army green da farar singlet inda tayi stocking singlet ɗin cikin wandon ta ɗaure da beld. Sai light green ɗin top wadda ta ɓalle duka maɓallanta ta barta a buɗe, Iskar da ake kaɗawa a gurin na diban rigar nata tana kamar zata cire,gaba ɗaya rigar tabar jikinta sai singlet

ɗin kawai, tsaye take daga jikin window na bedroom ɗin ta tayi crossing ƙafafunta suna a harɗe. Sosae iskar dake shigowa ta cikin window'n ɗakin ke mata daɗin shaƙa tare da ƙamshin flowering dake ata bayan window nan suke sake bata nishaɗi da jin cikakkiyar nutsuwa, saima taji ta nema ciwon kan data shigo dashi ta ne meshi ta rasa.♡ Shi yasa most especially Idan tana cikin yanayi mara daɗi idan bata son fita balcony takan tsaya a wurin ne ta yaye duka labulayen wurin nan take samun cikakken nishaɗi sosai.

☆

Lumshe fararen idanuwanta tayi tare da faɗawa wata duniyar ta daban, tunani take akan baya idan tace baya tana tunanin Baya cann da dadewa kafin rugujewar komi. A cikin idanunta dake lumshe komai daya faru yake dawo mata daki daki tamkar komai daya faru ne a waɗan can loƙutan haka komai ya Shiga zeroying mind nata. Saurin dawowa hayyacinta tayi sakamon zuciyan ta da taji tana son maido mata da hannun agogo baya, Bayan nan da har gaban abada bata fata da burin dawowarta cikin rayuwarta koda a matsayin mahaifin ne a gareta. Domin mahaifiyarsa ta rigada ta gama ɓata komi tun a wancen loƙacin. A yadda ta tashi ta tashi ne ta buɗe Ido da shi, Shi ne mutum na farko data fara ƙira da pa'apahh...........

Akan shi ta fara koyan magana tana yima kowa ƙyuwwa amma banda shi ciki kuwa har da Maamah'nta. Domin matukar Meesherh tana wurin juraij bata yarda da kowa bata kuma zuwa wurin kowa se pa'apahh'nta juraij. Ta kai ta kawo ko bacci zatay se da shi a gefenta, shi ke maga wanka ya wanke mata fufu idan tayi, ya goye ta a gadon bayansa da zani irin yanda uwa kewa ɗan ta, a loƙacin shi yana da shekaru sha bakwai a duniya ita kuma tana da 1 year's a cikin duniyar, Shi ne ya Renata yaci kashinta yaci fitsarinta har zuwa sanda ta shekara biyar a duniya, A kuma daidai loƙacinne abubuwa suka soma Sanja kansu, suka kuma soma samun saɓani wanda shi ne farkon jinin tubalin da har ya kai su ga irin wannan matakin da suke kai a yanzu. ♡

Duk wasu ɗabi'iu kalan nashi take yi masu kyau a da can baya kai takai ta kawo ko cima bata cin abinda baya ci, iyaka abinda pa'apahh'nta yake ci itama shi take ci. Saɓanin farko da suka fara samu a cikin rayuwarsu shi ne tun da ta ɗan ƙara wasu shekaru a cikin shida zuwa tara/goma ya fuskanta ita ɗin mayyar jin kiɗe-kiɗe da waƙe waƙe ce, ga shegen son kallon tsiya a wurin ta kamar me, duk yacce zeyi don ganin ya cire mata hakan abin yaci tu ra. Har yakai ga ya dena shiga lamuranta na wasu ƴan loƙuta haka zata zo ta shige jikinsa tayi ta masa koke koken banza har se ya dawo ya kula ta, Amma hakan bazai hana gobe ta sake kunna casunta ba, haka zata sa ata sawo mata irin kayan indiyawa sune kayan sawanta. Ya tattare ya ƙone amma haka Maama zata sake sawo mata wasu. Kai har takai ta kawo Meesherh ta dena shiga cikin duk wasu lamura na Juraij ta dena tsoronsa ta dena ƙiransa da sunan data bashi na pa'apahh wanda a da yayyenta shi kuma ƙannensa koda mutum ne yay kuskuren ƙiran sunan shi da sunan da ita kaɗai take son take ƙiransa da abinda to kuwa ranan wunin rigima zata wuni tana yi. Amma se gashi sannu a hankali komi nasu na sake samun saɓanin ra'ayi.

Se kuma a karo na biyu loƙacin da ya fahimta Film ta karanta, wannan shi ne tushen komi...

Shi ne tubalin dayay sanadiyyar rugujewa da watsewar komi don a nan ne Mahaifansu suka samu babban saɓani na farko kowa ya nuna nashi na shi ne. Daga nan komi ya tsaya musu cakkkk kowa ya fita a rayuwar kowa fita wacce suke jin fita ce ta har gaban abada abadan.

☆

★Wani gauron numfashi ta kawo me kyau lokacin data tuno kaɗan daga cikin wani sashi na

rayuwar da suka shuɗe na baya. Tsaye ta miƙa daga zaunen data kai gefen bed nata zuciyarta na wani kalan bugu very slowly ta miƙe. Waƙar (pareshanura ) ta cikin film ɗin Dhruva na jarumi _Ram Charan_ Wacce sukai da _Rakul preet_ ta kunna tana ƙure volume ɗin. Waƙar na sata shiga wani yanayi mai wuyar fassara tare da ɗebe wan can tunanin nata tana ta rawa tana juyi abinta. Ita ta bari on repeat tayi ta kuma dawowa daga nan ta koma waƙar *BAD BOY* ta cikin film ɗin _Saaho_ wacce jarumi _Prabhas_ tare da _Jacqueline fernandez_ kai da kaga yacce take rawan zaka tabbatar da cewan ehhhhhh lallai wannan dole a ƙira ta da TA DABAN ɗin, don kai tsaye kai baka isa cewan ba ita ne ta hau waƙoƙin ba kai tsaye bare kai duba da kalan shigar dake jikinta. Shigowan Maamah'nta shi ne ya katse ta don loƙacin 11:30 na dare harya gota. Kwantar da ita Maamah tayi bayan ta tofeta da adda'an bacci,seda ta ƙara kamar 15 minute kana ta fita a daƙin a tunaninta bacci Meesherh'n ta samu, sedai bata sani ba idonta biyu tana fita ta tashi zaune wani abu na mata suka a cikin zuciyarta. Wanda take yawan jin hakan a da a yanzu ma shike ƙoƙarin gaza control nata.

☆Around 11:30.

Kwance take saman ƙayataccen bed ɗin ta da ya gama jin haɗuwar duniya da kuma wani irin gyara na musamman, kai ba kace Mutum ne me Numfashi ke rayuwa a gadon ba.
Ɗan juyi ba da yawa ba tayi kaɗan kafin Ahankali ta shiga ware sleeping eyes nata da suka mata wani kalan nauyi kana kuma suka ƙanƙance, dishi dishin da take gani acikin su ne ya sanya ta maidasu ta kulle, sosai taji kanta na wani kalan bala'in sara mata, wanda take da ta cikakken tabbacin rashin baccin da bata samu ba ne a daren jiya ya haifar da hakan. dan haka take jin gaba ɗaya jikinta yayi weak haɗi da kasalan jiki ga kanta da taji ya dawo mata da wani kalan fitinannen ciwo. Hannu tasa tana ɗan dafe kan dake mata ciwo kaman zai rabe biyu,still idanunta masu kama da na mashayiya ko kalan like irin wanda aka janye su ɗin nan, Ahankali ta ɗan motsa jikinta tare da soma ƙoƙarin ɗaga kanta da takejin yayi mata nauyi sosai,jingina bayanta da jikin fuskar gadon tayi tare da sakin ajiyar zuciya tana miƙewa da ƙyar tare da nufar bathroom ɗin dake cikin bedroom nata. Shower kawai ta sakarma kanta tare da tokare hannuwanta duka biyu da jikin toiletry ɗin. haka ruwan shower'n ya shiga dukan jiki da kuma kanta, jin numfashinta na neman sarƙewa ne ya sanya ta janye jikinta da ƙyar. idanunta da suka sha ruwa sosai ta buɗe tana furzar da ruwan cikinsu. Ahankali ta ziro fararen sawayenta daga cikin bathroom ɗin, Sanye da rigan wanka ta fito komi ahankali takeyinsa, Anutsenta tazauna gaban mirror kan stool, blow drying gashin kanta tayi tai parking nashi a ƙasan ƙeyarta, ta ɗauki wasu sprays masu tsada da ƙamshi ta feffesa ma gashin,kai tsaye ta nufi wurin clothing nata da jibgin kayanta ke ciki, walking slowly take tafiyan fuskar nan babu walwala samm ko kaɗan a saman kyakkyawar fuskar tan,Bakar doguwar rigan Arabian jallabiya ta mata ta sanya. Hannunta riƙe da car key.
Bata tarar da Papiey'n taba ya fita wurin aiki amma kafin ya fita seda ya leƙata a loƙacin tana bacci kasancewan se dab da asuba bacci gwanin iya sata yay nasararn sace ta. Maamah na kallonta ta tabbatar ba lafiya ba. Zama tay a kusa da Maamah ɗin tana furta
"Maamah kaina kamar ze fashe ciwo ciwo ciwoooo yake min sosai!!!" Saurin tarota jikinta Maamah ɗin tayi jikinta harna rawa wajen furta "Subhanallahi amma kuma shi ne kika kwana a haka? Meesherh har yaushe kike son zanci gaba da miki magana akan lafiyar jikinki?" Se

kuma ta ɗan numfasa tare da furta "Shi ke nan tashi muje Hospital don ni ban woni yarda da cewan azo gida a duba ki ba  nima  duk yau haka haka nake ji ma wllh ba daɗi"  tsaye ta miƙe a sanyayen itama tana furta "A ahh Maah kiyi zaman ki bara yanzu zanje na dawo IN SHA ALLAH"

"Ke Meesherh anya kuwa duba fa yanayin ki sosai baki da lafiya kidai bari ko driver ne yayi driving naki" Dan murmushi tayi tana ficewa da tsokanar Maah ɗin. A Parking car na gidan suka haɗu da shi kallo ɗaya ya mata ya ɗauke kansa yana sake jin bugun zuciyarsa da fitowan nata. Akan Idonsa ta shige car nata tayi reverse tana janta tare da barin gidan ba tare data ko kalla inda yake ba.

Cikin nitsuwa shima ya shige tashi motar sanye yake da fararen kayansa kamar kullum. Security's ne suka hanzarin buɗe may mitar ya shige personal person ɗinsa na jan motar suna barin gidan.

Dummmmmmm haka yaji zuciyarsa ya buga shan kwanar da zata sada su da inda suka nufa ganin dandazon mutane fiye da dari kewaye a wuri guda. Cikin bugawar zuciya ya bama driver umarnin su tsaya. Cikin kamala da tattako ya nufi wurin cikin cikakken takun ƙarfi na hasali zaka san cewar ehhhh lallai shi ɗin Matashi  ne mai ji da lafiya irin ta da namiji, se hakan ya ɓoye yawan shekarun sa don idan ka kallashi befi ka bashi irin  35 year's ɗin nan ba a duniya, nan kuwa yakai 55 year's a duniyar. Kowa dake wurin ya gaza taɓa komai dake wurin se jinin dake malala ta ƙarƙashin motar data kife kirif da duk wanda yake a cikin ta. Wani irin jiri yaji ya ɗauke sa lokacin da idanunsa sukai masa arba da car ɗin kokkomeɗe a wurin.

Chakkk yaji numfashin sa ya tsaya amma yay ƙoƙarin taro shi domin bazai iya taɓa barin nashi numfashin ya fita ba tare daya tallafi Tata rayuwar ba.....

😔😔😔😔😔😔

_Innalillahi wa'inna ilaihi raji'un 3 meya faru? Meke shirin faruwa damu haka?_

The comments are dropping. 😔 ko dai baya muku daɗi ne? Naga ba comments ba reactions naku.

LPlease don't be a silent reader. Comment, vote and share. Thank you.

Love you all my mutanena ƴan Amana😘

_Put a smile on my face please. Vote, comment, and share My lovely friend's ana tare_

# Voice of the innocence
# Team Sheikh juraij

_Team juraij meke  meke shirin faruwa daku haka?_

_Laaaaa wayyoooooo wayyo wayyoooooo Meesherh ɗin mu😳😳😳😳_

*BY AMMEY LAYLERH ✍️*

07085041758